


# Kula da Matalauta

*Yesu ya ɗauki talaucin mu domin mu sami yalwar Sa*



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Jiya, mun dubi halaye huɗu marasa ƙyau da suke da dangantaka da kuɗi. Duk da haka, akwai wani halin da ya zama dole ne mu yi taka tsantsan wajen guje masa, wanda shi ne rashin kulawa da talakawa. Littafi Mai Tsarki ya yi mana gargaɗi a sosai game da rainawa ko cin zarafin talakawa.

Akwai Ayoyi da yawa na Littafi Mai Tsarki a kan wannan batu, amma za mu dubi ayoyi da dama daga cikin Misalai:

> "Wanda ya rena makwabcinsa zunubi ya ke yi, amma mai jin tausayin matalauta farin zuciya ke gare shi." (Misalai 14:21)

> "Mai jin tausayin fakirai yana bada rance ga Ubangiji, kuma za ya saka masa da alherinsa." (Misalai 19:17)

> “Wanda ya toshe kunnuwansa ga jin kukan talaka, shi kuma za ya yi kuka, ba kwa za a ji shi ba." (Misalai 21:13)

> "Wanda ya bayar ga fakirai, ba za ya rasa ba, amma wanda ya kawar da idanunsa za ya sha la'ana da yawa." (Misalai 28:27)

> "Mai adalci ya kan lura da da'awar talakawa, mugu ba shi da fahimi da za ya san ta ba." (Misalai 29:7)

Waɗannan ayoyi—da wasu makamantansu—sun ɗora mana babban nauyi na nuna kulawa ga buƙatun matalauta. Alama guda na zama adali shi ne kula da damuwowin matalauta. Akasin haka, alamar mugunta ita ce mutum ya kawar da idanunsa daga wahalar da talakawa ke ciki. Bugu da ƙari, an yi alƙawarin samun lada idan an kula da matalauta. Idan muka ba matalauta, Sulemanu ya gaya mana, muna ba Ubangiji rance ne. Lokacin da Ubangiji zai biya bashinmu, ba zai mance da ribar ba!

Na gode maka, Yesu, saboda aikinka a kan gicciye. Ina furta cewa zan kula da buƙatun matalauta, zan kuma kula da su,

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

domin Yesu ya ɗauki talaucina domin in sami yalwarsa.
Amin.

**Abincin Yini ★**

Kwafi: WD-B097-132-HAU
Sabuntawa ta karshe: 09 Sept 2026
Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources




© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.